Bismillahir-rahmanir-raheem

AURE KO YIN KISHIYA

Tattarawa:

Abbati Mai shago falgore

TSARAWA/HADA PDF:

Muhammad A salis Al'shekawiy

Rubutuwa:

Baban Manar Al'qasim

AURE DA YIN KISHIYA

Wannan batu da ganinsa zai ba ka dariya, ta yadda aka samo wani bambanci tsakanin aure da yin kishiya. Mu maza a wurinmu abu guda ne, kowa yana cikin farin ciki ne tsakanin ango da jama'arsa da dandinsa, haka ita amaryar.

Sa6anin yin kishiya, in da aka sami qarin wani 6angare a saman ango da amarya, wato 6angaren uwar-gida, wace ita da jama'arta suke cikin baqin ciki, wani lokaci mata sukan je taya kuka, akan sami abin da suke kira Dannan Qirji da sauransu.

A wannan sabon shiri muna so ne mu ba da wani magani mai suna HANA KISHIYA, sannan mu yi qoqari kuma mu duba wadan da suka riga suka sami kishiyar, suma mu ba su wani maganin wanda zai taimaka musu wajen zama lafiya a tsakaninsu da kuma jagoran tafiyan wato Maigida.

Wannan sabon shiri zai taimaka mana matuqa wajen gano dalilin da suke sa namiji ya yi tunanin qara aure, da hanyoyin da za a taimaka masa wajen cimma burinsa ko a daqile hanyar kuma a sami lada a wurin Allah!!

Ina gayyatar duk wata mace da take da abota da ni wajen bin wannan shiri tare da gyara kura-kuren da za a iya samu a gaban Jama'a, ina sa rai da watsuwar wannan shiri a shafuka daban-daban na facebook, Allah ya sa mu dace.

Hausawa suka ce "Ido wa ka raina?" Ya ce "wanda nake gani kullum" wannan ya nuna yawan ganin abu a kowani lokaci yana rage tsananin bukatarka da shi, don yanzu ya riga ya zama jiki kullun kana ganinsa. Kenan abin da ya kamata masoya su gane illar rayuwa cikin soyayyar da aka yi ta kafin aure, da lahanin da take yi wa rayuwar zaman auren.

Idan kuka lura, an gina soyayyar gabanin aure ne cikin qarya, bishiyar qarya kuwa fure take ba ta 'ya'ya, kowani lokaci namiji ya yi niyyar zuwa wurin budurwa, yakan qure adakarsa ne, ya wanke Goma ya tsoma Biyar, ga uban turare kafi-sallama, wata qila ya riqa aron motar abokansa, kayan sakawa ma yana iya aro don kada ta riqa ganinsa da riga guda, aljuhunsa kullun bai rabuwa da Nera, ta sa ce ko kuwa bashi ya yi, dan abu kadan ya yi murmushi, tare da fito da kyawawan dabi'unsa gami da rufe munanan.

Ita kuwa budurwar, da zarar ta san da zuwansa, za ta kimtsa kanta, ta yi duk wasu shafe-shafe da zai canja sifarta, kyaunta ya fito sarari sosai, ita ma turare yana yawo ko ina, da ta iso wurinsa sai fari da murmushi na kada zuciya, cikin murya mai taushin gaske, irin wanda Allah ya hana a Suratul Ahzab, sannan ta zauna kusa da shi ba bu muharrami kuma ga jikkuna suna gugar juna, daidai da yadda Annabi ya ce asha mutum da musulla ya fi ya ta6i matar da ba ta sa ba.

To anan an gama hada duk wasu shika-shikan sha'awa, kowa qoqari yake yi ya sami dan uwansa, sai duk tasirin da muka ambata su bayyana na qauna da bege, soyayyar ta yi ta burge wanda bai san a kan abin da aka gina ta ba, haka za a tafi har a daura aure, ko kuwa shedan ya yi aikinsa, su san juna kafin auren.

Da zarar an daura aure, zai fara ganinta da surar da ba ita ya saba gani a da ba, ba ya jin wannan qanshin, muryarta ta ainihi za ta fito, yanzu kowani kaya tana iya sakawa kafin ta yi wanka, sannan kullun yana ganinta kuma a kowani lokaci, bugu da qari bukatar da yake ta yaqin nema yanzu ya samu. Shi kuma in qaryar kudi yake yi yanzu za ta gani, in aron kaya yake yi duk zai bayyana, da haka komai yake rage qarfi sai a ce babu soyayya a halin yanzu.

Shi ya sa addini ya tsare wannan gaggawar, ya hana irin wannan soyayyar maras dawwama, ya saka al'umma a kan hanya ta qwarai yadda za a fara soyayya madawwamiya cikin halasci.

Namiji kowani lokaci kafin daura aure, ya saba ganin fara'a, murmushi, fari, da sauransu, ita kuwa macen ta saba duk wani motsi ta yi sai an tambaye ta dalili, da ta dan yi fushi a ba ta haquri, duk abin da ta nuna tana so sai an kawo mata koda kuwa ba'a take yi, irin wannan kulawar za ta sa ta fara tunanin amince masa da cewa zai iya kare ta daga duk wani abin da zai iya zama barazana daga rayuwarta, sannan yanzu ma kenan kafin a yi aure sai abin da ta ce, idan kuma ya shiga hannu ai sai yadda aka yi da shi matuqar shi ma buqatarsa tana biya.

Irin wannan yaudarar ta rayuwa wace sha'awa ke diban masoya kafin aure, iyaye sun dade da saninta, shi ya sa wani lokaci za ka ga ana ta dauki ba dadi tsakanin iyaye da 'ya'yansu, wata qila iyayen yaron sun san tarbiyyar gidan yarinyar, sun san cewa ko an yi auren ba dadi zai ji ba, haka iyayen yarinyar, me yiwuwa iyayen sun gane cewa duk bula ne ko an yi auren ba wani dadi za ta ji ba, sai su toge kan cewa sai dai ta fito da wani, a dalilin soyayyar da aka fara gita a wannan bigiren da bai dace ba, 'ya'yan ba za su ta6a ganin abin da ake nuna musu ba.

Ni Baban Manar na ta6a gaya wa wata yarinya cewa ta kar6i wanda ubanta ya za6ar mata kawai, domin abin da ya hango ko ta hau rimi ba za ta iya hangowa ba. Da bude bakinta sai ta ce : "Wallahi ni ma abin da na hango ko ya hau jirgi ba zai hango ba" galibi irin wannan aurarrakin in an gama moran juna sai ka ga an fara nadama, saurayin ya ce wallahi bai san haka take ba, ita kuma ta kasa magana don sanin badaqqalar da aka kwasa da ita kafin auren.

Kenan akwai hikima matuqa wurin da Annabi ya fadi dalilan da suke sa muke auran mata, in ka lura da kyau za ka ga wadannan dalilan ne suke sa matan su aure mu, kenan umurnin na mu ne mu Biyu, Annabi yana umurtanmu ne mu duba mai addini, ba mai dukiya, ko dan wane ba, ko mu duba qyalqyalin jiki da tsarin halitta, don wadannan sukan gushe nan da nan amma addini yana tare da mai shi.

Da wannan nake janyo hankalin 'yan uwa, a fahimta, akwai bambanci tsakanin mai addini da mai ilimi, Annabi dai cewa ya yi Zatuddini, bai ce zatul ilmi ba, don ba ko wani mai ilimi ne na gari ba, a cikin maza ko matan, bin cike shi ne gaba, amma barin iyaye su fara fadin ra'ayinsu abu ne mai matuqar mahimmanci.

Soyayya takan yi ta yawo tsakanin zuciyoyi ne, kuma a cakude take da tausayi ta yadda ba ka iya raba su sai in soyayyar ba ta amsa sunanta, masoya Daya daga cikinsu kullum zuciyarsa tana kan Dayan, zai iya ba shi abinci shi ya kwana da yunwa, zai iya lullu6e shi a lokacin sanyi shi ya haqura, zai iya faranta masa rai bayan shi a ciki yake da baqin ciki.

Mukalli Ummu Sulaim yadda ta sadaukar da darajarta ta mace mai dangi a kan furta kalmar shahada kawai, danta ya rasu, ta manta da zafin da take ji don kar zuciyar mijinta ta 6aci, ta yi abinci ta yi wanka da kwalliya ta ba shi kanta, duk a shirye-shiryen gaya masa dansa ya rasu, don dai kada ransa ya 6aci, duk qoqarin faranta rannan da ta yi na ta a 6ace ne, amma ta kar6i baqin na ta don farin na mijinta, in ba soyayya ta ina za ka ga zuciya tana tafarfasa baki na fidda tausassar murya, fuska tana murmushi, ido yana fari, qwaqwalwa tana tunanin yadda za a gaya maka halin da ake ciki ba tare da taka zuciyar ta damu ba?

Irin wadannan matan ba a samunta dazarar tasha ado da sallah, ko ta yi wankan maraice, kuma ba ta samuwa don matsayin

ubanta ko dukiyarsa, takan samu ne wajen bincika dabi'unta da tarbiyyarta, ka nemi macen da kullum tana cikin yi maka addu'a ne, wace ba ta damu da abin hannunka kamar yadda ta damu da zuciyarka ba, kullun cikin binciken inda kake da rauni ne don ta qarfafaka.

Dubi Ummu Salamah matar Abu Salamah kafin ta auri Annabi, yadda ta yi ta kuka na tsawon watanni har sai da iyayenta suka rabu da ita ta koma wurin mijinta, ku dubi Zainab 'yar Annabi SAW yadda Annabi ya raba ta da mijinta lokacin bai muslunta ba, yadda ta yi ta qulle-qullen da har sai da ya muslunta ya mai da ita.

Dubi Uwar muminai Khadija RA, wace Annabi bai iya yin aure ba duk da tsufarta, har sai da ta rasu, ya aure ta da girmanta amma ta yi masa 'ya'ya shida, hatta sunanta mata sun yi kishi da shi, Khadija ta koyar da mata yadda ake riqon namiji RA, to haka ake soyayya ta qwarai wace kowa a shirye yake kuma a kowani lokaci ya biya wa masoyinsa buqata, har qoqari yake yi ya san matsalarsa don ya yi maganinta kafin ya ambace ta, babban burinsa ya ga kwanciyar hankalin abin qaunarsa.

Kai kuwa mai zuwa kullun dare wajen budurwa, qar yar yau daban ta gobe daban, wace iriyar rayuwa kake so ka qulla, ka daura soyayyarka gaba daya a kan sha'awar jima'I, ya kake tsammanin soyayyar bayan buqatarka ta biya? Me ya sa ka yi sha'awar aurenta, shin natsuwarta ce ko addininta? Tarbiyyarta ce ko dabi'unta na qwarai? Maganar gaskiya kyau shi ne a gaba wajen

za6en mace a yau, shi ya sa a yau kwalliya a mota ba qauyanci ba ne, shigar banza da nuna tsaraici ba abin damuwa ba ne don ba albarkan auren ake nema ba.

Abin da ya kamata mutane su gane shi ne, soyayyannan fa ibada ce idan aka yi ta yadda ta dace, ka saka zuciyarka cewa don Allah kake yi ba don kalan mutum ba ko sifarsa ko danganensa da tarin dukiyarsa, kana yi ne don addininsa, kamar dai yadda Khadija ta so Annabi don amanarsa, sannan Maisara ya ba ta labarin duk abin da ya gani tare da Annabi SAW, sai ta tabbatar cewa mutunne da bai kamata ta bari ya ku6uce mata ba.

Zahiri, Khadijah RA in kudin Annabi za ta duba yaron gidanta ne, in shekarunsa za ta duba, ta haife shi, in iliminsa za ta duba, ita ta riqa karatun Attaura shi kuwa a lokacin bai iya ko rubutu da karatu ba, amma ta aure shi kuma ta miqa masa wuya gaba daya sai abin da yake so shi za a yi, wanda ba ya so kafin ya yi magana an watsar da shi, sai ta zama soyayya ce sabo da Allah da addininsa, ba soyayyar kyaun jiki da tsarin halitta ba ne, an gina ta ne bayan aure, kuma don Allah SW, Annabi yana cewa a Hadisin Qudisi: Allah SW yana cewa:

أين المتحابون بحلالي اليوم أظلهم في ظلي يوم لا ظل إلا ظلي

Ina masu qaunar junansu don daukakata? Yau zan inuwanta su a inuwata, ranar da babu wata inuwa sai ta wa.

Muslim ya rawaito

Don haka Khadija da girmanta na shekaru haka ta ba da dukiyarta don hidimar addini, ita kuma ta duqufa hidimar mijinta, ba abin da zai daga masa rai sai ta yi qoqarin gamawa da shi kafin ya sani, da haka yake zuwa kogon hira, duk da ba ta son rabuwa da shi amma takan qara masa guziri, tarihi ya dauko mana irin qoqarin da ta yi na kwantar da hankalinsa ya yin fara saukan wahayi.

To ashe Khadija RA ba ta yarda da tsufanta wajen gajiya yi wa Annabi hidima ba, kalli yawan 'ya'yan da ta haifa masa, har ta rasu Annabi bai qara mata ba, bai kuma yi niyyar qarawan ba sai da sahabbai suka matsa da ya auri Saudah,tun da yanzu bai da mata, bacinnan, hadisai sun nuna ya auri mataye amma bai daina yanka rago yana raba wa qawayen Khadija ba, ashe kenan tsufar mace ko rasuwarta ba sa janye soyayyar namiji gare ta, gajiyawarta ce ta fito da soyayyar asali, da tsayawa qyam wajen yi masa hidima, da gyara kai, da miqa masa wuya duk lokacin da yake so, da nuna masa shirin ba shi abin da zai bukata a duk lokacin da ya nema, da rashin damuwa da abin hannunsa, ko zantukan wani a kan matar, da haqiqance cewa duk abin da mijin zai yi ba zai sa macen ta rage abin da take masa ba, don ba don shi take yi ba don Allah ne, wadannan su suke tsare son mace a zuciyar namiji.

Idan muka lura za muga, duk wahalar da mace za ta sha, shi ne zai dada raunana zuciyar namiji zuwa gare ta, kwadayi da wayau, ko nuna kwalliya da wayewa, ko girmam iyayenta da jami'o'in da ta yi karatu ko inda take aiki, suna da tasiri wajen sa namiji ya so mace amma na lokaci ne iyakantacce, soyayya madauwamiya ita ce wace aka gina domin Allah, da yi wa miji hidima, ga ta da riba a duniya da lahira.

Haka yake a bayyane cewa Allah SW ya yi halitta kala Biyu mace da namiji, ya dora namijin akan macen, cikin mutane har zuwa dabbobi, in kuka lura da tsarin dangogin kyanwa da na kare zuwa tsintsaye za ku ga mace tana bukatar namiji wajen sauqaqe rayuwarta ta jin dadi ko ta kariya, a cikin mutane ma haka yake ko da muslunci ko babu, macen da ta za6a wa kanta cewar ba za ta yi aure ba, to dole ta yi zamankanta da sunan 'yanci, amma kuma duk wanda ta so shi ko ta so abin hannunsa, yana iya juya ta yadda yake so, haka dai za ta yi haquri da shi don an jarabce ta da shi ko abin hannunsa.

Maganar gaskiya Allah SW ya halicce mu, ya kuma dorawa namiji sha'awar yin aure, don haka aurensa zai yi kamar yadda dabi'a ta sauqaqe masa, ko dai auren fari ko qari, ba wani dalili da yake banbancewa;mutum yakan yi aure ko qari don sha'awa, neman gamsuwa, neman haihuwa, buqatar da namiji, neman hutu ko kwanciyar hankali, biyan wasu buqatu, cika alkawari, bin iyaye, hada zumunci, tausayi ko taimako da sauransu.

Babu wata mace da za ta sifantu da duk sifofin da namiji yake bukata ta yadda za ta gamsar da shi wai kar ya yi mata kishiya, in har da maganin hakan, to sai dai kar ya fita waje, kar kuma wani ya shigo masa, duk yadda ka lissafo dalilan yin kishiya guda Goma, wani zai ambato wasu Goman ba tare da ya ambaci na ka ba.

To yanzu meye mafita? To sai dai mu fara binciken wasu dalilai wadan da za su sa namiji ya ji tausayin mace, ya dubi hidundumun da take yi a cikin gida, ya ga bai da buqatar qarin aure da kansa, amma ba wai matar ta yi wani abu da zai hana shi ba, a duk lokacin da ta yi qoqarin hana shi ta wasu hanyoyi, qara qarfi zai yi, idan har ta ci nasara a wani wuri, to ba shakka zai nemo wani wurin, me yiwuwa kuma gwara wurin farko a wajenta.

Allah ya hore wa mace hanyoyi da dama, wadan da inda za ta bi su, ba shakka duk wani namiji a hannunta yake, zai iya yin kuri da hargagi, amma sikiyarinsa yana hannunta kuma tana iya juya shi yadda take so, sai dai fa abin da nake so mace ta gane, ita ma kafin aure ta ga abubuwa da dama, don haka wannan amaryar lokacinta ne za ta dawo kamar yadda take, don haka makaman da za mu ambato su za ta nemo in ba ta da su.

A duk lokacin da kika sami kanki a matsayin matar aure, to ki yarda da sunan da ake kiranki da shi na uwar gida, ki mai da hankali kan cewa mai gidan da duk wani da yake qarqashinsa na ki ne, ki bude masa zuciyarki gaba daya, ki tilasta masa fahimtar cewa (a aikace ba da baki ba) ke fa amfaninki a gidannan shi ne kwanciyar hankalinsa da farin cikinsa, ya kamata ya gane cewa, gidansa wajen hutunsa da jin dadinsa ne, ta yadda duk lokacin da ransa ya 6aci to ba magani sai in ya dawo gida, duk wani nau'I na fara'a, fari, murmushi, sassanyar murya, kusanta, yauqi, kisisina, shagwa6a, turare, taimakawa, hikima wurin magana, qanqan dakai, girmamawa, shawara ta gari, da miqa wuya, duk na sa ne kuma a lokacin da yake buqatarsu, ya kamata ki nuna masa cewa adonki, rayuwarki, hidundumunki da na 'ya'yanki duk suna

hannunsa ne, kuma dama na sa ne.

Kar ki yarda ki saka wa ranki cewa taimakonsa kike yi, a'a, aikin wahalar da kike yi sabo da Allah ya ce ki yi ne, ba wai don kina matsayin matarsa ba, in kika dauka a matsayin matarsa, haqiqa duk lokacin da ya 6ata miki rai, wani abin ba za ki yi ba, wata mata (Allah ya jiqanta) tana ba ni labarinta ta ce, ta tuna wata rana da ta yi jinkirin abinci sabo da ruwan sama, mijinta ya falleta da mari, tana kuka amma tana qoqarin saurin gama masa abincin kamar yadda yake buqata, duk da cewa akwai lema itacen ba ya kamu, ta ce: Abin mamaki matan yau, wai in miji ya ba su haushi suna iya barin yi masa hidima.

Ki dauki cewa duk lokacin da kika sami kar6uwa a wurin mijinki, Allah zai kar6e ki, matuqar ba ki iya kwantar wa mijinki rai to ba ki cika mace ba, to ina ga ke kike ta da masa da rai? Kar ki yarda hankalinsa ya tashi ki kasa kwantar masa da shi, to ina ga ke kike ta da masa da shi? Kada ki yarda ya dawo gida cikin baqin ciki ba ki kawar masa da shi ba, to ina ga ke kike fitar da shi daga gida sabo da 6acin rai.

Da yawa wasu mata suna zaton dafa abinci, kwanciyar aure, haihuwar yara, reno, yi na yi- bari na bari shi ne aure, tabbas wadannan abubuwan su ne masu sauqi wurin zamantakewa, amma duk macen da ta kasa gamsar da mijinta cewa ita ce hutunsa, ita ce aljannarsa ta duniya, rumbun ajiyar amanarsa, sikiyarin tuqa rayuwarsa tabbas tana da saura, kuma ba da jimawa ba za su zama su Biyu ko Uku ko ma Hudu, gwargwadon lalacewarsu da rashin sanin yadda ake gudanar da rayuwa.

Uwargida ba na son na ce sakacinki ya sa maigidanki yake qoqarin yi miki kishiya, don namiji idan ya so aure, rashin dalili ma wani dalili ne mai qarfi wanda zai yi aure a kansa, kuma a kai zai dage har sai ya isa zuwa ga cin ma burinsa, sannan matuqar ya yi niyya, da wahala a sami wani mahaluki da zai iya hana shi, tamkar dai yadda ya yi niyyar yin auren fari.

To amma ki dubi kanki ki gani, shin kin tsare wasu abubuwa wadan da ya kamata a ce mace ta yi su? Wani lokaci kikan yi qoqari amma ba a inda ake buqatarsa ba, misali yi wa miji kwalliya irin wace za ta ta da hankalinsa, amma sai ya zamo yana sha'awar lalle, ke kuma ba ki so don haka ba ki yi, ko kikan yi abin ci mai dadi da zai burge kowa amma shi ba ya son ya ji ko gishiri mai yawa, ke kuma ba ki ga yadda za ki yi abinci ba yaji ba ko a ce gishiri bai ji ba, ko kuma ki sa wani kalan magi da ba ya so, kikan ba shi kanki a matsayin ta sa, amma shi akwai lokacin da yake buqatarki, ke kuma ba za ki iya ba sabo da wasu ra'ayoyi da ba za ki iya barinsu ba, ko kina girmama shi na qarshe, amma ba ki da mu da iyayensa ko 'yan uwansa ko abokansa ba, irin wadannan abubuwa sukan sa ki ga kina wahala wajen yi masa hidima amma bai ko kallon abin da kike yi, sabo da a ganinsa ba ki yin su a yadda ya kamata.

Sannan ki duba ki gani, in ya shigo gida shin kikan bar komai nan take ki haro shi da murmushi da barka da zuwa, ko kikan bari sai ya shiga daki ne sannan ki bi shi? Shin kikan kar6o kayan da ya shigo da shi ki biyo shi a baya ko kikan zura masa ido ne? In zai fita kikan raka shi har qofa ko kikan dake a daki ne? Kin saba

masa da yin masabaha dake ko ba ki ta6a kwatantawa ba? Kikan fesa turare a jikinki in ya shugo don yasan don shi kika fesa ko ba ki yi? Kikan zauna kusa da shi in zai ci abinci ko kikan aji ye ne ki fita? Kikan yi qoqarin tattauna maganganu masu mahimmanci da shi ko kina jira shi ya nemo ki da zance?

Wasu abubuwa kike yi na girmama mahaifansa? Shin yana da tabbacin kin dauki iyayensa kamar na ki ne? Shin kin kama 'yan uwansa a hannu? Ko kin yi qoqarin sake wa 'yan uwan ta yadda in suna son wani abu a hannunsa za su biyo ta wurinki? Shin kin yi qoqarin nuna masa cewa qaunarsa kawai kike so ba abin hannunsa ba a aikace ba a baki ba? Shin yana da amincin cewa ke ce asusun asirinsa na magana da na dukiya? In babu wasu hanyoyi kika bi wajen samun hakan?

Da yawa mace gaggawa take sawa ta rasa abin da ya kamata ta samu, so da qaunar namiji ga mace suna iya raguwa da zarar rashin yarda kowani iri ne ya ratso tsakiya, misali ya fara fahimtar ba shi kike so ba abin hannunsa ne, ko shi kadai kike so ba ki damu da na sa ba, ko kuma iyayenki da 'yan uwanki sun fi na sa, ko kuwa wasu qananan abubuwa.

QANANAN ABUBUWA KAMAR YA???????

TO ME YA SA MAZA SUKE QARA WA MATARSU KISHIYA??????

Uwargida akwai wani abu mai mahimmanci da ya kamata ki gane, don an ce wane malami ne, bai isa a ce shikenan ya san yadda zai yi soyayya da ke a cikin gida ba, haka don an ce wane dan gayu ne, bai zama dalilin da za ki sami duk soyayyar da kike bukata ba, wannan ya damfara ne kacokan a kan binciken dabi'unsa da kika yi kafin ki yarda ya mallaki zuciyarki, idan duk wannan kashe dakalin da kuka yi ta yi bai agaza miki wajen saninsa ba, ko kin shigo gidansa sa6ani za ku yi ta samu.

Subhanallah, kyawawan mata su suka fi kowa shan wahalar aure a cikin mata, kamar yadda wani lokaci malamai sukan sha wahala wajen samun mata na gari, dalili kuwa, 'yan matan da suka fito da kyaun fuska, a kan yi ta ruwan kudi a kansu, sau da yawa wanda ya fi arziki shi yafi samu, gwargwadon sakin hannunsa, to irin wadannan ba su da lokutan matansu, kuma sun fi kowa neman kintsattsun mata da kyawawa, bar batun soyayya hatta zaman hira da iyalinsu ba su da lokacin yin sa, suna iya kawo mata duniya gabanta amma kar ta nemi hakkin auratayya a wurinsu, wasu irin wannan ba ka raba su da dan leqe-leqe, su kuwa matan ana ganin ta sami komai na duniya, har ka ga mata suna sha'awar su zama kamarta, amma ita kadai ta san halin da take ciki, a hakan kuma zai dauko mata kishiya.

Malamai kuwa, ko sun koyar da yaran dauke su ake yi, sabo da ba su da kudi, wani lokaci sai ka ga an kawo musu wasu yaran wadan da ba su suka koyar da su ba, wani lokaci sai a yi ta samun taho mu gama a tsakaninsu, sai ka ga a waje yake malami amma

a gida sai a hankali, abin da yake hana galibin mata zama lafiya da mazajensu shi ne qarancin bincike akan yadda rayuwar za ta kasance bayan aure, ba su cika lura da dabi'un saurayi kamar lurarsu da abin da yake ba su ba, shi ya sa nadama take da sauqin faruwa.

To ko ya lamarin yake dai, ke mace idan kika ce ba za ki saba da kalmar (yi haquri) ba, ke ce za ki sha baqar wahala, da yawa mata sukan ce "Ai tunda ya yi kaza ni ma kaza zan yi!" Ko "Tun da ya yi kaza ni ma kaza zan yi" duk mai wannan dabi'ar ta shirya zama da kishiya, sannan za ta sha mamakin yadda zaman zai kasan ce, amma lallai ki zama mai haquri, ki iya shuka damuwarki ko kya girbi farinki nan gaba, sai dai namiji sunansa kenan namiji a ko'ina yake.

TO WAI, YA ZAMA KENAN SAKACIN MACE ZAI SA A YI MATA KISHIYA????

Uwargida zan so ki fahimci abu guda daya, duk lokacin da mutum ya gaji, ba wani abu mafi dadi a wurinsa kamar hutu, wasu mazan sukan dawo gida a gajiye ne sabo da wahalar neman halas, to wasu matan ba su da fiqihun zama da miji, a daidai wannan lokacin za ka ga sun kawo masa abinci kuma suna qoqarin dole hira za su yi da shi, wanda in bai kula su ba, ya zama abin zargi, a irin wannan lokacin yana shigowa ki tarbe shi cikin fara'a da nuna jin dadi na sake haduwa da shi, ki taimaka masa ya yi abubuwan da ya saba yi da zarar ya shigo gida, in ya yi nisa da cin abinci sai ki matso kusa da shi, don ba shi bayanan da yake buqata, in kika

ga yana jin barci to kar ki matsa masa da hira, ki ba shi shawarar ya kwanta, ki dada gyara masa wurin kwanciyar duk da yake a gyare yake, ko ba komai dai ya ga kwaskwarimar da kika yi a jikinki, ga kuma qanshinki yana ta ratsa shi.

Idan bai da niyyar kwanciya ki lura da shi, in kika ga yana da wani aiki da zai yi, ki taimaka masa har ya fara aikin, kuma ki nemi yara su bar shi ya huta, in kuwa kika ga ba ko Daya to wannan damarki ce da za ki zauna da masoyinki abin qaunarki, uban 'ya'yanki kuma wanda ya maye makwafin iyayenki wajen kula da lafiyarki da mutuncinki da duk abin da ranki yake so.

Kada ki matsa da yi masa maganganun soyayya, sau da yawa ba sa amfani a irin wadannan wuraren, ki yi qoqarin nuna masa ne a aikace, yadda zai gane cewa ke ce fa hutunsa in ya gaji, kece fara'arsa yayin da ransa ya 6aci, kece gatarsa kuma a shirye kike wajen yi masa hidima a duk lokacin da yake bukatarki, ki nuna masa cewa ke fa mace ce, kuma a dakinsa sannan halaliyarsa, ba kamar mazan da ya yi ta ma'amalla da su ba ne a waje.

Ki san me kike gaya masa, da wace murya kuma kike magana da shi, wasu irin kalmomi kike amfani? Ki tabbatar da yaranki kin koyar da su sanin lokutan magana da mahaifinsu, da lokutan zama da shi don kada su riqa 6ata miki timetable, ki sani in kika bar su hakan zai iya haifar miki da sakamakon da ba shi kike so ba.

Ma'ana yi wa yara tsari zai baki damar jifar tsuntsu Biyu da dutse Daya. Na farko dai hakan zai baki damar biyan buqatunki ke da mijin na ki cikin sakewa da jin dadi. Na Biyu zai taimaka wajen taqaita tunanin samun sabuwar mace wace ba ta da yaran da za su riqa taqaita masa bukatunsa a lokacin da yake matuqar nenansu.

Akwai zafi matuqa ka dubi matar malam Bahaushe ka ce ba ta iya soyayya ba, ma'ana zaman auren ma kana so ka ce da ka kawai take yi, ba ta ma san me take ba, wannan kam ba wata Bahaushiya da za ta yarda da shi, kowacce za ta dubi kanta ta qaryata ka, ko ta dubi zagayenta ko matattararta, duk dai za su taimaka mata wajen fitar da ita daga zargi mai matuqar girma.

To amma me ya sa matan Hausawa da na Fulani sun fi kowa zama zawarawa a wannan Nahiyar ta mu ta Afurka? Je ka kutuna ka ga Fulani masu qoqarin raba aure, je ka gidajen Hausawa ka za6i Bazawarar da kake so, kafin dan lokaci kai ma ka sako ta! Tabbas akwai matsala a wani wuri, ko dai mazan ne ba su san yadda za su riqe matan ba, ko kuwa matan ne ba su iya riqe mazan ba, kowa dai yana zargin dan uwansa, don ko zawarawan ba su tsira ba, abin da ake cewa, "kowa ya ga godiya da sirdi wani ta kayar!"

To ke don mu kar6i hujjojinki don me kika yarda da cewa "Namiji ba dan goyo ba ne" me ya sa kika amshi cewa "Duk wace ta dauki miji a matsayin uba za ta mutu marainiya?" Me ya sa kika

tarbiyantar da 'yarki kan cewa in aka riga aka yi aure soyayya ta qare saura haquri? Yaushi kika fara tarbiyantar da 'yarki yadda za ta zauna da miji? Wani abu ne na soyayya yake faruwa tsakaninki da mijinki wanda kike ganin 'yarki za ta dauka ko ba a koya mata ba? Tun yaushe 'yarki take koyon zaman aure? Wani qoqari kika yi ta yadda 'yarki za ta fahimci cewa ita fa kashi na Biyu ne a gidan mijinta ba taimakonsa take yi ba? Shin kin koya ma ta a dabarce cewa ba a iya mallakar jikin namiji da harshensa da aljihunsa sai an mallaki zuciyarsa da qwaqwalwarsa

To dai za mu iya cewa matar malam Bahaushe ta fi matan duniya qwaqwalwa don haka ba sa koya wa 'ya'yansu wadannan abubuwan sai lokacin zuwa dakin miji ko wataqilama a ranar da za a kai amaryar daki, ko kuwa ta fi sauran sanin addini shi ya sa kunya take hana ta koya wa 'ya'yanta wadannan abubuwan har da mahimmancinsu oho, wata ko girki sai ta kusa aure take koya wa 'yarta, shi ya sa da wahala ka ga sun hana tara zawarawa a gidajensu.

Koda yake ba za a daura wa mata duk wadannan laifukan ba, amma tsarin malam Bahaushe mace take tarbiyar 'yarta, wannan ya sa aka sami Hausar da take cewa "Cutar 'ya mace ta uwarta ce" duk kuma wata budurwa uwarta take kira, ba uba ba, kenan wasu matsalolin har da rashin ilimi, don mace tana jira namiji ya koya mata wasu abubuwa ne, a daidai lokacin da yake matuqar buqatarsu gareta, kamata ya yi ta shigo da kayanta gaba Daya, kenan "In dai 6era yana da sata to lallai daddawa tana da wari".

KO KIN FAHIMCI WANNAN?

*Y*a kamata uwargida ki yi mamaki mai matuqan girma, ta yadda ga ki kyakkayawa son kowa qin wanda ya rasa, ga ki 'yar dangi, duk wata halitta da ke fitar da kyawun mace kina da ita, kin tabbatar da cewa za ki iya fitinar duk wani da namijin da kike so, sai dai tsoron Allah ya hanaki, amma abin mamaki har da irin wannan haduwar, mijinki yana neman wata wace ko kusan kama qafarki ba ta yi ba a komai kuwa, anya ba tsafi a ciki kuwa? Tabbas akwai!!!

Koma baya! Lokacin da kike budurwa kullum kyawunki qaruwa yake yi, shigar yau daban ta gobe daban,hoda kala-kala kin sansu, jikin madubinki kwalabe ne na turare daban-daban, da na manshafawa mai fitar da sura,a fagen murya kuwa ga magana cikin sanyin murya, wani lokacin ma ki tsiri wata shagwa6a ta ba gaira ba dalili, ba wani sa6ani da zai taso muku sai ma sha'awar saduwa da take qaruwa duk ranar Ubangiji, shin wadannan abubuwa na ki sun canja ko yadda maigidanki yake ganinki cikin ado da qanshi da fara'a da fari ko shagwa6a tun kafin aure har yanzu haka kike?

Mun yi imani cewa ba wata mace mummuna a duniya sai wace ba ta iya ado ba, ko ba ta iya magana ba, in muka lura, sabo da kadaitaka, da damuwa, Ubangiji ya halicci Hauwa'u ga Adam AS don debe masa haso.

Dubi tsarin halittunmu, in kyau mutum yake nema sai dai ya dauki mace, haka dadin murya, da laushin ciki, da haqurin ko jimirin hadiye matsaloli, da saurin haddace abubuwa don taimakon mijinta, shin matanmu suna aiki da wadannan abubuwa kamar yadda ya kamata?

Wata za ta ce maka iyayenta ba su turota bauta ba, kuma wadannan abubuwan ba shakka suna daukar hankalin namiji sosai da sosai, in mace ba ta yin su a cikin gida don gamsar da maigidanta ba, abu ne mai sauqin gaske idonsa ya hango su a wajen wata budurwar kafin ta shigo ta daina ya sake hango wata, ba macen da ba ta san abin da zai janyo hankalin maza gare ta ba, to ki sani, abin da ya shigo da ke, shi fa zai sake shigowa da wata.

Za ka yi mamakin yadda mace take masifar qin kishiya, alhali ba wani abu da ta yi wanda zai hana mijin ganin kyawun wata, shiga malamai ko bokaye ba shi ne mafita ba, wanka da gari ba ya maganin yunwa sai an sha.

Abubuwan da muke rasa ganewa ko na ce mata suke gaza iyayenta sun yi digiri a kanki ba, zai yi wahala su qyale ta ta yi ta bandarwa ba tare da bibiyar yadda kuke rayuwa ba.

Wani lokaci abin yana da ban mamaki ta yadda za a ba da labari game da abin da kika yi da wanda ba ki ma san da shi ba, wannan sananne ne cewa, in namiji ya yi niyyar aure duk rigimar uwargida ba za ta hana ba, duk kuma abin da kika yi yana komawa gidan amaryar tare da qarin gishiri, a maimakon ki ci gaba da abin da ba zai yi miki amfani ba, gwara ki haqura ki zuba wa sarautar Allah ido, kar ki yi hargagin da a qarshe zai zama miki abin magana.

Iyaye sukan yi wa 'ya'yansu hudubar cewa "ke ma fa mace ce kamarta, don haka kada ki nuna kina jin tsoronta, don in ta hauki ba za ki ji da dadi ba" da haka za a lissafa mata irin dabi'unki, da kuma yadda za ta 6ullo miki, kenan in ta shigo ki yi qoqari ki qaryata wannan ilimin na ta, ta wurin ma'amalla mai kyau, kar ki kuskura ki nemi jin ra'ayinta game da ke, ko abin da aka gaya mata a gida.

Me yiwuwa an yi mata qarairayi, to nuna mata kyawawan dabi'u zai sa ta qaryata abubuwan da aka gaya mata a hankali, ta ce ita kam ba ta ta6a ganin haka ba, amma lokacin da ta shigo da zafin kai ke ma kika ce duk a hadu a lalace tabbas qarshe ke ce za ki zama abin magana a bakin mata.

In kika yi amarya, ki yi qoqari ki nuna mata abubuwan da ba ta sani ba, kuma ki yi qoqari ki kau da kai a kan wasu abubuwa da za su iya faruwa, sabon abu kowani lokaci yana da ban sha'awa, yana da daukar idanu, akan nace masa har sai ya zama jiki, mukan ce "sabo sabo ne ko da sabon kashi ne" a don haka ki dan yi haquri har ita ma ta zama jiki, ki tuna ke ma kin bi wannan yanayin, wanda da wahala ta sami abin da kika samu.

A duk lokacin da kika amshe ta hannu bibbiyu, kika ci gaba da ma'amalla da ita tare da jajja da baya da take yi, a hankali za ta tabbatar cewa ba za ki cutar da ita ba, koda kuwa an zugo ta da farko, in kika nemi ku zauna lafiya to kowa zai ji dadi, amma bin ta a hankali ba ya nufin kina jin tsoronta, ai durqusa wa wada ba

gajiyawa ba ce, in kika farauci zuciyar amaryarki da dabi'u na qwarai nan gaba sai abin da kika ce za a yi, to ya za a yi ki farauci zuciyar namiji zuciyar mace ta gagara in ba rauni ba?

Duk mace tana da gaggawa wajen yanke hukunci kafin ta yi bincike, wanda wannan yakan zo ne sakamakon dogararta a kan zuciya 100%, alhali qwaqwalwa ma tana aiki a jikinta, kusan ga6ar da ta fi aiki kenan a jikin mace, wato qwaqwalwa, amma duk lokacin da wani abu ya taso mata, to takan yi fatali ne da duk wani abin da ya shafi qwaqwalwan ta yanke hukunci gwargwadon abin da ya yi wa zuciyarta dadi, albashi daga baya ta yi aiki da qwaqwalwar wajen fahimtar ta yi kuskure tare da nemo hanyoyin gyara, da yake qwaqwalwarta tana aiki sosai, da wahala ka ga ba ta samo hanyar gyara ba, koda yake wannan ba zai hana a sake 6allo wata rigimar gobe ba, matuqar zuciyarta tana bugawa.

Irin wannan lamarin ne ya sa mace ba ta da wata dorarriyar masoyiya a cikin kishiyoyinta, da yawa mata sukan hada kai ne gwargwadon bukatunsu, misali: Akan sami tsama mai matuqar muni tsakanin kishiyoyi guda Biyu, sabo da uwargidan ba ta iya jure wasu abubuwa da take ganin wariya ce da muganci irin na mai gidan, sai ta yanke hukuncin cewa gwagwarmaya ita ce kawai mafita, to a lokacin da ta ga za a yi wata matar, takan wayance da cewa ita ba ruwanta kwarinta za a wa kishiya, domin idan kwarin ta dauki kishi, ba shakka uwargidan za ta sami sauqin janyo ta a jiki su hada kai don fuskantar amaryar.

Wannan ya zama dole a wajen uwargida, don idan ta ci gaba da jan zare, to ba shakka ta ba da dama kenan kwarin ta hada kai da

amaryar, qarshe kuma ita ce za ta shiga Uku, don wariyar takan dawo kanta ne, in haka ta faru kuwa, za ta iya yaba wa aya zaqi, sabo da wadancan sabbi ne, wata qila hajarsu ta fi kasuwa wurin wanda ake nuna masa.

A cikin irin wannan zara fi, mata ta Uku in budurwa ce ya kamata ta yi qoqarin nuna rashin fahimtar abin da yake faruwa a cikin gidan, har sai ta gano matsalolin da kanta, bai kamata ta dogara da maganganun da ake gaya mata a waje ba, don haka ba zai mata dadi ba, muddin ta shiga da shirin fada da kishiya, tabbas ta dada bude qofa ne na haduwar sauran matan a kanta, wata qila kuma ta dan sha wahala kafin ta gano wasu sirrika na gidan.

Sai dai ba shakka wace za ta zo ta Uku kar ta yarda ta nuna musu cewa ita ma fa ba kanwar lasa ba ce, ta bi su a hankali, wata qila ba masu son rikici ba ne, ta iya yiwuwa dabi'ar mace ce kawai ta san zama ita kadai, in kuwa ta same su masu tsananin kishi ne, to ta fahimci cewa duk inda wuta takai da zafi ruwan sanyi yakan yi maganinta, ta yi qoqari ta raba kansu wajen yi musu ladabi tare da share abin da suke yi.

Wannan hanya da ta dauko in ta dage a kai, kowace za ta tuno abin da ya riqa faruwa tsakaninsu su Biyu, wata qila wannan ya sa ta fara jin tsoron kada fa dayarsu ta ha'inceta tunda dama soyayyar ba ta Allah ba ce, wannan zai iya kawo sauqin abin.

Amma ke amarya ka da ki yarda rigima ta fara tasowa ta wurinki, masamman da yake ke ce suke ganin fitina wace za ta tarwatsa gida, ki dan yi haquri har jama'a su fara maganar abin da yake

faruwa tukun, ki sani duk wata cutarwa da za a yi miki, wani qarin qarfi ne gare ki da kuma hujjoji a gaban mai gidanki, shi ma yana kaso mai girma wanda zai sa mai gidan ya dada sonki da tausayin ki da qoqarin kare ki.

Wata rana ina koyar da wasu larabawa sai wata malama a cikinsu ta tambaye ni wai mu a Nigeria me muke kiran sakakka? Na ce Bazawara, ta ce to wace mijinta ya mutu fa? Na ce Bazawara, sai mamaki ya cika ta, ta yadda muke kiransu da suna Daya, sai ta ce, wace ta girma ta rasa miji fa? Sai na ce ai mu ba mu da wannan matsalar sai ta ce "Amma ina yi muku barka!"

A nan qasashen Larabawa sai mace ta kai shekara 45 ba tare da wani ya taya ba, galibin biranensu mata kan yi aure ne a shekara Ishirin da doriya zuwa Talatin da qari, sabo da qarancin mazan masu nema, har ta kai dole mai neman miji ta riqa fitar da ga6o6in sha'awarta ko za ta samu ta fitini wani ya taya, duk in da aka ce akwai biki to ba shakka rukunnan bala'o'I sun gama haduwa a can.

Duk wata macen da mijinta ya mutu, in ta yi sa'ar gaske ta sami wani dan uwanta da zai shigar da ita kafin shekara 6 zuwa 10, sabo da 'yammata ma ba su sami shiga ba bare kuma zawarawa, ita kuwa wace mijinta ya sake ta, in ba sa'a ba, ita da aure har abada, shi ya sa suke da suna don banbancewa, 'yanmatan kuwa galibinsu auren zumunta ne, dan kawu ko dan baffa, don dai a samu a yi maganin matsalar da take tasowa.

Duk da mummunar kaciyar da ake yiwa matan don kashe sha'awarsu ana dai samun shaggu a gidajen marayu, kuma galibinsu a gida aka same su, duk wadannan bala'o'I suna bayan wasu matsaloli ne da suke nuna qarancin mazan:

1)Tsadar sadaki, da wasu bidi'o'I da aka zagaye auren da shi, ta yadda mutum ba zai iya aure ba sai ya yi shekaru yana tara kudin da za a kashe a rana Daya ko wasu 'yan kwanaki qalilin, da kuma abubuwan da za a saya wa amaryar na qarya.

2)Auren mace Daya ba kishiya, mu da muke yin mata 2 ko 3 ko 4, har yanzu ga matannan sai dai in baka nema ba, to ina ga masu auren mace Daya kacal, ita ma bayan ya tsufa? Wannannan rashin yin kishiyar ko na ce rashin qara aure sai ya zama fitina a matattarar Larabawa gaba Daya, dalili kuwa shi ne:

A)Larabawa suna yawan yaqi ga bama-bamai suna kashe maza a ko'ina, matansu suna zama zawarawa, 'yammata kuma suna rasa maza, da za a riqa auren koda guda biyu-biyu wata qila a rage.

B)Hatsarurrukan da suke faruwa a kan hanyoyi galibi maza ne suke mutuwa, don su ne matafiya.

C) Yaqe-yaqe da rashin kwanciyar hankali, da rashin samun lafiyayyen abinci a wasu wuraren sai ya zamo yanzu mata ake haihuwa sama da maza, kenan akwai buqatuwar yawan mazan da za su aure su.

Shi ya sa duk lokacin da na duba qasarmu sai na ga (AURE KO YIN KISHIYA) ya taimaka wajen rage bala'o'in da matattararmu za ta iya fadawa.

ALHAMDULILLAH

MAWALLAFI BABAN MANAR ALQASIM

TATTARAWA ABBATI MAI SHAGO FALG

TSARAWA DA HADA PDF MUHAMMAD

A SALIS AL-SHEKAWIY